NAZARIN YADDA MARUBUTA KAGAGGUN LABARAI SUKE AMFANI DA ALJANU DOMIN CIM MA MANUFOFINSU NA WALLAFA

Mustapha Kallamu
School of Continuing Education
Bayero University, Kano
Dept. of Arts and Humanities

Tsakure

Wannan bincike ya yi nazarin yadda marubutan ƙagaggun labaran Hausa suke amfani da aljanu a matsayin dabarar adabi domin cim ma manufofinsu na wallafa. An duba yadda ake amfani da aljanu wajen gwada jarumai da isar da saƙo cikin sauri da taƙaita ko tsawaita labari da taimakon taurari da gina salo da tsoratarwa da kuma bayyana siffofi da halayen aljanu. An gudanar da binciken ne ta hanyar nazarin wasu zaɓaɓɓun ƙagaggun labarai kamar *Ruwan Bagaja* da *Magana Jari Ce* da *Gandoki* da *Aljani Ya Taka Wuta*, tare da amfani da ra'in ƙyallaro al'ada (Referential Theory of Culture). Sakamakon binciken ya nuna cewa amfani da aljanu wata dabara ce ta fasaha da marubuta suke amfani da ita domin sauƙaƙa warware matsalolin labari da gina salo da kuma jan hankalin masu karatu. Binciken ya kuma tabbatar da cewa aljanu sun kasance muhimmin ginshiƙi a adabin Hausa tun daga tatsuniyoyi har zuwa ƙagaggun labarai na zamani.

1.0 Gabatarwa

Hausawa sun daɗe tare da aljanu waɗanda suke kira da iskoki ko mutanen ɓoye. Sun yi imani da cewa aljanu wasu halittu ne masu halaye da ɗabi'u waɗanda suke na daban da na ɗan'adam. Mutanen ɓoye su ne, Hausawa 'yan bori suke kira aljanu waɗanda suna da iko na musamman na rikiɗa zuwa siffofi da kamanni da halaye iri-iri. A wasu lokuta sukan fito a sifar mutane ko dabbobi ko macizai ko ƙwari ko iska irin ta guguwa. Sannan Hausawa sun yi imani da cewa, aljanu suna da wata mallaka ko wani iko a kan mutane.

Sani (1982) ya yi bayanin yadda aljanu suke ya ce, "Aljanu sun kasu kashi biyu, akwai fararen iskoki su ne masu taimakon mutane. Kana su ne iskoki da suke kawo arziki ko wani alheri. Daga cikin su akwai Malam Alhaji da Bafillatana da Ɗangaladima da Uban dawaki da Sarkin rafi. A ɓangare na biyu akwai baƙaƙen iskoki, su ne masu kawo sharri da

hauka da talauci. Daga cikin baƙaƙen iskoki akwai Duna da Uwar Gona da Baƙo da Kure da Danko da Nakada da Gajimare da Bakangizo".

Haka nan, Bunza (1995) ya ce "Ana samun iskoki a ko'ina a sararin samaniya a jeji a tsaunuka da kuma a jikin ɗan'aam da kuma garuruwan da mutane ke zaune a ciki".

Wannan ya nuna cewa ana samun aljanu a ko'ina a cikin Duniya. Bayan wanzuwar Musulunci sai Kur'ani ya yi bayanin ko su wane ne aljanu inda Allah (S.W.A) yake cewa "Ban halicci mutum ba da aljanu sai domin su bauta mani".(Suratul Jinn). Haka nan wannan Aya tana cewa "*Kuma ya halitta aljani daga bira, daga wuta (Suratul Rahman 15)*

Wannan bayani da Allah ya yi game da aljanu sai aka gane cewa, su aljanu ba abin bauta ba ne, su ma halittu ne da aka halicce su da wuta. Amma domin su bauta wa Allah. Ashour (1983) ya yi bayani a kan Aljanu inda yace, "su Aljanu an halicce su daga bira ta wuta wato wuta mai kama da wutar lantarki. Haka nan ya yi bayanin cewa, "Aljanu sun kasu kashi uku. Na ɗaya su ne nau'in aljanu da suke tafiya cikin iska wato su ba su zaune wuri ɗaya. Sai kashi na biyu su ne aljanu mazauna gidaje wato waɗanda suke zaune a ƙauyuka da garuruwa da birane kuma suna zaune da sarakunansu. Sannan kashi na uku su ne aljanu mazauna gidaje, wato suna zaune ne tare da mutane a ɗakuna da masallatai da ramuka da cikin soraye.

Tasirin aljanu a kan al'adun Hausawa ya samo asali ne tun farkon lokacin da Hausawa suke bauta wa dodanni da duwatsu da aljanu Kallamu (1996). Domin a ciki tatsunyoyi da almara da labarai aljanu na taka muhimmiyar rawa. Amfani da aljanu a cikin matani na adabi, wata tsohuwar hanya ce da sabuwa a wajen gina ƙagaggun labarai. Domin akwai wasu ayyuka da ɗan'adam ba zai iya gudanarwa ko aiwatar da su a cikin labari ba, sai dole an yi amfani da aljanu domin labarin hankali ya yadda da shi. Misali mutum ya je bangon duniya cikin ƙanƙanen lokaci ko shiga ƙarƙashin ƙasa da zama wata halitta, wato rikiɗa. Waɗannan halayya ce ta aljanu, kuma ko mutum ya yi bajinta irin wannan za a ce yana hulɗa da aljanu. Haka nan idan an yi maganar wallafa, ana magana ne a kan ƙagaggun labarai.

1.1 Ma'anar Kagaggen Labari

Labarai ne waɗanda ake ƙirƙirawa domin ilimintarwa da faɗakarwaa da nishaɗantarwa a rubuce ko a maganance.

Ibrahim (1992) ya ce “Kagaggen labari shi ne shiryayye kuma a cikin hikima da fasaha wanda ta bayyana ma’anoni na rayuwa”. Wannan ma’ana ce da take nuna cewa ƙagaggun labarai su ne masu bayyana wasu al’amura da suke faruwa a cikin al’umma na sharri ko na alheri. Sannan Yusuf (2002) ya ce “ma’anar ƙagaggun labarai su ne labarai da mawallafi ya shirya da ka, sannan ya rattaɓa shi a zube”

Haka nan Mukhtar (2002) ya ce “rubutun zube ana nufin rubutun da ba waƙa ba, kuma ba wasan kwaikwayo ba. Zube ana nufin tsagwaron rubutu wanda aka yi shi a cikin shafuka da layuka”.Saboda haka ƙagaggun labarai kamar hoto suke ɗauka na wasu al’amura da suke faruwa a cikin al’umma, su rubuta su.Haka nan wannan bincike ya ta’allaƙa ne a kan hanyoyin da marubuta suke bi su yi amfani da aljanu ƙagaggun labarai domin cim ma manufofinsu na wallafa.

1.2 Tarihin Samuwar Kagaggun Labarai

A ƙasar Hausa an fara samun nau’in rubutu na Yunananci a ƙasar Kano sai dai wannan nau’in rubutu ba shi da inganci. A farkon ƙarni na bakwai Larabawa suka fara shigowa ƙasar Hausa domin yin kasuwanci da yaɗa addinin Musulunci, sun koya karatu da rubutu da kuma koya nazarin litattafai. Daga nan ne aka fara koyon rubutun wasiƙa. Manyan malamai da dama sun shigo ƙasar Hausa irin su Al-maghili da Al-suyiɗi da Wali ɗan marna da Wali ɗan masani. A shekara ta 1890 Turawan bincike suka fara shigowa ƙasar Hausa daga nan sai Turawan mishan sai na mulkin mallaka daga nan suka kakkafa makaranttun boko. Sai buƙatar litattafai na karantarwa suka taso. Turawa suka fara rubuta litattafai irin su ka koyi karatu na Rimmer R. East. Sai *The Six Hausa Plays* na R.M East. Sai *The Hausa Dramatic Literature* na Mr. Adolf Rudiuf. Daga nan sai ‘yan ƙasa suka ɗauka irin su *Magana Jari Ce* da *Karamin Sani Kukumi* na Abubakar Imam. Sai *Ganɗoki* na Bello Kagara da sauran ɗimbin littattafai.

Sannu a hankali rubuce-rubuce suka yi yawa waɗanda ake rubutawa domin samar da nishaɗi da karantarwa a manyan makarantu da ƙanana. A shekara ta 1980 aka fara samun litattafai na Adabin Kasuwar Kano (AKK) waɗanda suka ƙunshi jigogin soyayya da kasada da jarumtaka da kasuwanci da nisiha da gargaɗi. Da tafiya ta yi nisa aka fara mayar da labaran finafinai.

2.0 Yadda Mawallafa Kagaggun Labarai Suke Amfani da Aljanu Domin Cim ma Manufofinsu na Wallafa:

2.1 GwadaTaurarin Littafi da Aljanu

Taurarin labari su ne waɗanda ake amfani da su wajen isar da saƙonni a labari. Babban taurraro ba zai cika jarumi ba sai an yi masa gwaji ko jarabawa da aljanu. Ma fi ƙololuwar gwajin tauraro ita ce, a yi amfani da aljanu. Misali a *Magana Jari Ce* na II, a labarin Yusha'u na Rimi ba ka Fargaba. An gwada shi da aljanu a matsafar garin. Inda Sarki ya sanya aka kai shi ɗakin gumaka ya kwana tun da farko ya yi iƙirarin babu abin da zai razana shi a duniya. Misali, "Yana zaune sai ya ga cinya ta faɗo, sai kuma can ɗaya ta ƙara faɗowa, sai kai ya faɗo. Sai ya tashi ya ɗauki cinya guda ya jinjina ya ji babu nauyi. Ya ce, ashe ma wannan huhun ma'ahu ne ba shi da nauyi"(Sh. 50).

Haka dai aka yi ta gwada shi har gari yawaye babuabin da ya razana shi. Sai misali na biyu a littafin *Aljani ya Taka Wuta*. An gwada babban tauroron Naziru da wata aljana da ta tare hanya inda yake wucewa sai ya ga itaciyar tsamiya ta yi girgiza ta tumɓuko duk da jijiyoyinta ta nufo shi. Sai ya yi tsaye ƙyam yana kallonta. Sai ya ji murya ta ce "Kai jarumi ko to! Za ka gaya masu"(Sh. 101).

Haka dai aka yi ta ba shi tsoro da siffofi iri-iri. Amma bai razana ba. Waɗannan hanyoyi ne da marubuta suke amfani da aljaniu domin jaraba manyan taurarin littafi.

2.2 Isar da Saƙonni Cikin Sauri Kamin Kyaftawar Ido

Marubuta ƙagaggen labara sukan yi amfani da aljanu domin isar da saƙonni cikin sauri waɗanda ɗan'adam bai iya wa idan ma ɗa'adam ya yi wannan aiki za a ce, anya wane ba ya aiki da aljanu?. Wani abun idan an ce ɗan'adam ya yi su. Hankali ba zai yarda da hakan ba. Misali a labarin *Ruwan Bagaja*, aljanu sun ɗauki Alhaji babban tauraron cikin ƙanƙanen lokaci da wani kogi kafin ƙyaftawa da bisimilla sun kai shi ƙasar da zai ɗebo ruwan bagaja. Asali tafiyar shekaru zai yi, kafin ya je wannan ƙasa da ruwan bagaja yake. Misali, daga kogi zuwa ƙasar da ruwan bagaja yake tafiya ce ta shekaru amma aljanu sun ɗauke shi cikin ƙanƙanen lokaci sun kai shi wajen da zai samu ruwan bagaja (Sh. 45).

2.3 Taƙaita Lokaci da Tsawon Labari ta Hanyar Amfani da Aljanu

Mawallafa sukan taƙaita lokaci da tsawon labari ta hanyar amfani da aljanu. Misali a littafin *Ruwan Bagaja*, mai ba da labarin ya ce, tafiyar da Alhaji zai yi ita ce ta shekaru, amma an yi ta cikin ƙyaftawar ido, wato ɗan ƙanƙanen lokaci.

Abun lura da la'akari, idan da marubucin bai kawo aljanu ba tsakanin wannan kogi da Alhaji sai ya yi tafiyar shekaru kafin Alhaji ya je ƙasar da ruwan bagaja yake kuma labarin zai yi tsawo sosai kuma zai ɗau lokaci, amma sai ya taƙaita shi ta hanyar amfani da aljanu.

2.4 Taimakon Taurarin Labari Cikin Gaggawa

Mawallafa da dama suna amfani da aljanu wajen taimakon taurari cikin gaggawa. Misali a littafin *Maganar Jari* ta uku da ta biyu. A labarin Kamarzaman da labarin Amjadu da Ansadu an yi amfani da aljanu wajen taimakon taurarin. Sannan a littafin *Aljani ya Taka Wuta* daga ƙarshe aljanar tana taimakon babban tauraron Naziru. Sannan akan yi amfani da aljanu wajen fiddo da wasu matsaloli da kuma magani da kariya ta aljanu.

2.5 Alƙinta Salon Labari ta Hanyar Amfani da Aljanu

Salo dabaru ne na gina labari domin jawo hankalin masu karatu. Misali a littafin *Ruwan Bagaja* an yi amfani da aljanu wajen gina salo misali "Babu mai iya ɗaukar wannan ruwa sai Sarkin Aljanu". A nan abin da marubucin yake ya yi dabaru ne na marubuta. Domin da ruwan bagaja a hannun mutum yake da bai yi wuyar samu ba kuma labarin ba zai yi tsawo ba. Haka ma a littafin *Jiki Magayi* inda marubucin ya yi amfani da ƙaron kalgo kuma wajen samo shi ana cin karo da aljanu kuma ya nuna sai a ƙungurmin daji ake samun ƙaron kalgo. Wannan shi ne ya sanya labarin ya yi tsawo.

2.6 Amfani da Aljanu a Matsayin Taurarin Labari

Mukhtar (2002), ya ce taurari su ne mutanen da mawallafi yakan saƙo a cikin labarinsa. Kuma suna da yawa maza da mata da yara da dabbobi da tsofaffi a labarinsa. Amfani da aljanu a matsayin taurari, wata tsohuwa da sabuwar hanya ce da marubuta sukan yi amfani da ita domin ƙulla labari. Misali a littafin *Magana Jari* Ce akwai taurari irin su Kashi-kashi da Sarkin Aljanu da Doguwa da Zairaƙanu da Marƙayanatu da Kolin-koliya. Sannan aljanu suna fitowa a matsayin dabbobi ko wasu halittu irin su barewa da doki da zaki da kura (Sani 1982).

2.7 Tsoratarwa da Hora Taurari Masu Laifi

Marubuta ƙagaggun labarai sukan yi amfani da aljanu domin tsoratarwa. Misali a littafin *Gandoki* an tsoratar da Garba Gajere ɗan Gandoki da aljanu kuma daga ƙarshe an horas da shi da aljanu. A littafin *Jiki Magayi* (Sh. 25) mawallafin ya yi amfani da baƙin aljani a wajen koya wa wasu taurari darussa na rayuwa, wato babban tauraro Abubakar.

2.8 Mawallafi Kan yi Hikima Wajen Sanya Aljanu a Matsayin Masu Bayar da Labari a Cikin Fage

Mukhtar (2000), ya ce, shi mai bayar da labari daga cikin fage shi ne wanda mawallafin littafi yake sakar wa bayar da labari(Mukhtar 1999). Amma kuma ya sanya ido. A littafin *Magana Jarii Ce* ta biyu, a labarin Kamaruzzaman ɗan Sarkin Shaharzaman mai bayar da labari a bayan fage ya sakar wa wata aljana bayar da labarin mai suna Maimunatu inda take bayar da labarin ta gano wani ɗan sarki wanda duk duniya ba ta ga mai kyawunsa ba. Daga nan suka shiga gardama da wani bayan gidan su. Har daga ƙarshe aka ɗauko tashi wadda ya gano Badura aka kwatanta su wannan wata hikima ce ta mawallafa.

2.9 Fito da Tarihin Yaƙe-Yaƙe da Suka Faru ta Hanyar Amfani da Aljanu

Mawallafa sukan fito da tarihin yaƙe-yaƙe da aka yi a shekarun baya ta hanyar amfani da aljanu. Misali a littafin *Gandoki*, mawalalfin ya ui amfani da salon amfani da aljanu wajen ba da tarihin yaƙe-yaƙen da Umarun Nagwamutse Sarkin Kwantagora ya yi.

2.10 Fito da Dangantakar Mutane da Aljanu

Mawallafa sukan yi amfani da aljanu domin fito da dangataka da take tsakanin mutane da aljanu. A littafin *Gandoki* an fito da dangantaka ta sarauta da addinin da auratayya. Haka nan a littafin *Aljani ya Taka Wuta* an fito da dangantaka ta soyayya da zumunci. Sannan a *So Aljanar Duniya,* an fito da kishi tsakanin aljana Mugayya da babbar tauraruwar littafin *Bodado*.

2.11 Bayyana Siffofi da Ɗabi'un Aljanu

Mawallafa sukan yi amfani da aljanu wajen fito da siffofi da ɗabi'un aljanu. Yadda suke rikiɗa kamanni iri-iri kamar dabbobi kunami da macizai da zaki da kyanwa. Sannan ana fito da yadda suke rikiɗa itatuwa da siffar mutane. Misali a littafin *Aljani ya Taka Wuta,* aljanar da ta ba Naziru tsoro ta rikiɗa ta zama itaciya. A *Magana Jari Ce* ta biyu

labarin Yusha'u aljanu sun rika ba shi tsoro da sassan jikin mutum a matsafar da aka kai shi ya kwana.

2.12 Amfani da Aljanu Domin Tsawaita Labari

Mawallafa suna amfani da aljanu domin tsawaita labari. Misali a littafin *Ruwan Bagaja* marubucin ya yi amfani da salon a fadada labari ta hanyar amfani da aljanu. A inda ya kawo *Ruwan Bagaja* kuma babu inda ake samun shi sai kasar aljanu kuma kasar tafiya ce ta shekaru masu dimbin yawa. Sai kuma ya sake wata dabarar aljanu suka dauki babban tauraron a bakin kogi suka yanke masa wannan doguwar tafiya cikin kankanen lokaci suka kai shi kasar da *ruwan bagaja* yake.

2.13 Takaita Labari ta Hanyar Amfani da Aljanu.

Mawallafa sukan yi amfani da aljanu domin takaita labari ta hanyar daukar taurari a kai su wata kasa cikin kankanen lokaci kuma kawo wani abu cikin sauri. Sannan aljanu sukan kawo wani taimako cikin gaggawa kafin kyaftawar ido. Misali a labarin Kamaruzzaman, a inda aljanu suka dauke Badaru da Kamarazzaman cikin kankanen lokaci kuma kowannensu yana wata duniya suka hada su domin a kwatanta a ga wanda ya fi kyawo.

2.14 Bayyana Karfin Aljanu da Gajiyawarsu

A al'adar Hausawa kafin zuwan addinin Musulunci sun dauki aljanu ababen bauta ne, da Musulunci ya zo sai ya warware komai cewa aljanu su ma halittu ne da ake halitta domin su bauta wa Allah. A littafin *Gandoki* da *Magana Jari ce* ta biyu da *So Aljannar Duniya* da *Jiki Magayi*duk an bayyana karfin aljanu amma daga karshe an nuna gajiyawarsu. Misali, a littafin *Gandoki*ya yi yaki da aljanu ya ci nasara a kan su. Haka ma a littafin *Aljani ya Taka Wuta* Naziru ya yi jan hali ya nuna bai jin tsoron aljanu da sauran dimbin littattafai da suka yi amfani da aljanu. Domin nuna gajiyawar su da kuma nuna rashin karfin su

2.15 Fiddo da Wasu Magunguna a Labarai ta Hanyar Amfani da Aljanu

Mawallafa sukan yi amfani da aljanu wajen fiddo da wasu magunguna. Misali a littafi *Jiki Magayi* an fiddo da karon kalgo. A littafin *Ruwan Bagaja* an fiddo da *Ruwan Bagaja* da sauran litattafai kwatankwacin wadannan.

3. Ra'in Bincike

An yi amfani da Ra'in Kyallaro Al'ada, wato *Referencial Theory of Culture* domin zaƙulo wasu ɗabi'u da al'adu na aljanu da marubuta ƙagaggun labarai suke amfani da su domin cim ma manufofinsu na wallafa.

4. Hanyoyin da aka bi Wajen Gudanar da Bincike

An yi amfani da hanyoyi da dama wajen gudanar da wannan bincike daga cikin manya da ƙananan hanyoyin da aka yi amfani da su, sun haɗa da:

i. Ziyartar masana rayuwar aljanu
ii. Amfani da littattafai da suka ƙunshi rayuwar aljanu
iii. Amfani da ƙagaggun labarai da suka ƙunshi salon a amfani da aljanu domin su cimma manufofinsu na wallafa.
iv. Hira da masana rayuwar ɗan'adam da biladama.

5. Sakamakon Bincike

Dukkan bincike yana da manufa da dalilin da suka sanya aka gudanar da shi da kuma ire-iren fa'idojin da ƙudurori da ake so a cim ma wa. Sakamakon wannan bincike ya gano muhimman abubuwa da dama daga cikinsu akwai yadda marubuta suke amfani da hikimomi da aikinta labaransu ta hanyar amfani da aljanu. Domin akwai ayyuka da dama waɗanda dan'adam bai iya yin su sai dole. An yi amfani da ɗan'adam wajen gudanar da su. Misali kamar gwada ko jarraba taurari da aljanu da isar da saƙo cikin sauri da taƙaita lokaci a wajen ba da labari da tsawaita labari ta hanyar kawo wani aiki mai wahala domin labari ya yi tsawo da taimakon taurarin labari cikin gaggawa da alkinta salo da sauran ɗimbin hanyoyi da ake amfani da su domin gina labari. Babban sakamakon binciken shi ne, an gwada wannan sakamakon bincike a fagage daban-daban ya zama wani sabon babi da aka fiddo ga manazarta da marubuta.

6. Kammalawa

Amfani da aljanu ba a littattafai kawai ya tsaya ba kuma salon ya daɗe tun a labarai da tatsuniyoyi da almara da ƙissa da hikayoyi da waƙoƙi na gargajiya da wasanni irin su dambe da kokowa da bauta ta gargajiya da bukukuwa da adabi na zamani a wasanni na dandali da talabijin da finafinai na Hausa. Saboda haka wannan tsoho da sabon salon a amfani da aljanu, sabon fage ne da ya kamata a assasa shi ya zama wani kwas da za a rinƙa karantar da shi a makarantu.

MANAZARTA

Abdullahi, I. H. (1972), "Traditional Healers in the Kano City" a Discussion Paper Read at the Department of Islamic Studies, Bayero University, Kano

Abdullahi I.H (1977), Islama Medicine and Practitioners in Northern Nigeria: London: Edqin Mellen Press.

Abdullahi, A. (1980), Camfi a Kasar Hausa, B.A Project, Ahmadu Bello University, Zaria.

Ashour Mustapha, (1980), The Jinn in the Qur'an and Sunnah Dar Altaqwa Street,London.

Abubakar S.Y (1997), Bori a Zariya, M.A Dessertation, Bayero University Kano.

Adamu, T.A (1983), "Asalin Tsibbu Yaɗuwarsa da Tasirinsa ga Al'ummar Hausawa". Semina Paper, CSNL, Bayero University, Kano.

Alti, S.B (1989), "Maita a ƙasar Hausa", B.A project Bayero University, Kano.

Baba, A.T (1977), "Camfe-Camfe da magungunan Hausawa kan Tama", in HausaLanguage Literature and Culture, CNL, Bayero University Kano.

Bunza, A.M (1992), Magani Cikin Musulunci, Sidi Umar Press, Sakkwato.

Bunza A.M (1995), "Magungunan Hausa a rubuce: (Nazarin Ayyukan MalamanTsibbu)" Ph.D Thesis Vol. 1 – 3, Bayero University Kano.

Greenberg J. (1941), The influence of Islam on a Sudenege Religion J.J

Augustin Publishers, New York.

Hambali, M.J (1990), Maganin gargajiya na Afirka, Gaskiya Cooperation Zaria, Nijeriya

Madauci, 1 et al, (1968), Hausa customs, Zaria: Nothern Nigeria publishing com.